**Cluster Protection Niger**

# Strategie du cluster protection/ groupe de travail protection 2018, Niger

## 1 . Nazari a kan halin da ake ciki

Kasar Nijar na fuskantar matsaloli na tsaro a cikin jahar Difa mai fama da hare haren kungiyar boko haram da kuma wasu yankuna na jahohin Tawa da Tilaberi masu fama da hare haren kungiyoyin tayar da kayar baya da ke fitowa daga arewacin kasar Mali.Domin tunkara da shawo kan wadannan matsalolin,hukumomin kasar ta Nijar sun kafa dokar ta bace a cikin jahar ta Difa tun cikin watan faburairu na 2015da kuma cikin wasu gundumomi 7 na jahohin Tawa da Tilaberi a cikin watan maris na 2017.Daga watan yuni zuwa watan satumba na 2017 kimanin hare hare 50 kungiyoyin yan ta'adda suka kai a kasar ta Nijar;daga cikin wadannan hare haren an kai 28 a jahar Difa,18 a jahar Tilaberi,1 a jahar Tawa,da kuma 2 a jahar Agadas.Kashi 90 cikin 100 na mutanen da hare haren suka rutsa da su farar hula ne da suka hada da mutane 50 da suka rasa rayukansu,25 suka jikata, yayin da 57 aka yi awon gaba da su.A jahar Difa an hana gudanar da ayyukan noma, da sana'ar kamun kifi a wasu yankuna,sannan kuma an hana wasu harkokin kasuwanci tsalkanin jahar da yankin arewa maso gabashin Nijeriya yayin da aka rufe kasuwanni 16 a cikin jahohin Tawa da Tilaberi..Haka zalika gwamnatin ta Nijar ta dau matakin hana zirga zirga da babura a cikin jahar ta Difa da wasu yankuna na jahohin Tawa da Tilaberi,matakan da suka yi wa tattalin arzikin mutanen yankunan illa tare da jefa su cikin mawuyacin hali .

## Difa

Tabarbarewar tsaro a cikin jahar da kuma kasashen yankin tafkin Cadi ya tilasta ma wasu al'umomin jahar da na kan iyakokin kasashen kaura suna barin gidaje ko yankunansu .A kasar Nijar mafi yawan mutanen da suka kaura na zaune ne cikin jahar Difa da ke kudu maso gabashin kasar.Ya zuwa ranar 30 ga watan afrilu na 2017 an kididdige mutane dubu 127 da 299 da hare haren kungiyar boko haram suka tilasta ma tashi daga garuruwa ko yankunansu zuwa wasu yankunan na daban a cikin jahar.Sannan kuma an tabbatar da jahar na kunshe da yan gudun hijira dubu 106 da 146 da kuma wasu yan nijar dubu 14 da 546 da tashe tashen hankulan masu nasaba da boko haram suka tilasta ma gudowa galibi daga Nijeriya domin komowa gida.Ma'aikatar jahar Difa mai kula da tantance jama'a da bakin haure da kuma yan gudun hijira ce ta tabbatar da wadannan alkaluman.Mafi yawan wadannan mutanen na zaune ne a cikin sansanonin yan gudun hijira da aka kafa galibi a gefen hanya mai tashi daga Yamai,ta ratsa jahar ta Difa ta wuce kasar Cadi.Hare haren da yan kungiyar boko haram ke kaiwa daga nan zuwa can a kan iyakokin kasashen na ci gaba da kasancewa babbarbarazana ga wadannan al'umomin.Ba'idin wannan matsalar,akwai kuma dimbin damuwa da wadannan mutanen ke da ita game da ba su kariya da kulawar da ta dace.Kungiyoyin agaji da dama musamman hadin gwiwar kungiyoyin da ke kula da bayar da kariya da kulawa a Nijar tare da taimakon rukunin kungiyoyin agajin da ke aiki a jahar ta Difa,na gudanar da ayyuka a cikin jahar domin riga kafin duk wasu hadura da kuma kai ma al'umomin da ke cikin mawuyacin hali dauki.Rukunin kungiyoyin agaji da ke aiki a cikin jahar ta Difa ( GTP ) ya gudanar da wani aikin kididdiga a cikin watan afrilun 2017 domin tantance bukatocin jama'an da suka tagayyara a cikin jahar ta Difa.

Mafi yawan mutanen da suka bar garuruwa ko yankunansu a cikin jahar Difa,sun bar su ne yau da wani lokaci mai tsawo.Kashi 50 cikin 100 na sansanonin mutanen da suka tashi daga yankinsu zuwa wani yankin na daban a cikin jahar ta Difa,da kuma kashi 75 cikin 100 na sansanonin yan gudun hijira na kunshe ne da mutanen da suka baro garuruwansu na asali sama da shekara daya ( 1 ).Wadannan mutanen sun tsere ma tashe tashen hankula masu nasaba da rashin tsaro ne a cikin garuruwansu ko yankunansu na asali wanda shi ne babban dalilin da ya tilasta ma kashi 93 cikin 100 na mutanen da suka kaura a cikin jahar barin garuruwa ko yankunansu,sannan kuma shi ne ya sa kashi 99 cikin 100 mutanen da suka yi hijira barin kasarsu.Kaurar da jama'a ke yi daga nan zuwa can tana da yawa.Wasu mutanen na kaura ne su koma wani wurin da ba ya da nisa da garinsu na asali,kamin daga bisani su kaura zuwa wani wurin mai nisa da garinsu na asali idan ya zamanto yanayin rayuwarsu ko na tsaro ba mai kyau ba ne.Yan gudun hijira sun fi wadanda suka tashi daga wannan wuri zuwa wancan a cikin jahar ta Difa yawan kaura,watakila saboda nisan da ke akwai tsakanin garinsu na asali zuwa sansanin da suke zaune,ko kuma tabarbarewar yanayin tsaron da yankin nasu na asali yake ciki.

## Hadurran da ke hujjanta bayar da kariya da kulawa

Galibi mutane na kaura ne sakamakon munin tagayyarar da suka shiga a cikinta.Ta haka ne matsalolin tsaro kamar hare hare da kuma al'amurran keta hakin dan adam kan zama ruwan dare so tari,ko kuma su rika faruwa jefi jefi. Ire iren wadannan matsalolin kan shafi kashi 43 cikin 100 na mutanen da ke cikin sansanonin wadanda suka kaura daga garuruwansu zuwa wasu yankuna na daban a cikin jahar ta Difa,sannan kuma sun shafi kashi 46 cikin 100 na yan gudun hijira. Duk da haka adadin hare hare da sauran isgilin da ke faruwa ya rage a cikin mafi yawan sansanonin da kididdigar ta shafa idan aka kwatanta da yadda lamarin yake watanni uku baya kafin a yi kididdigar.Galibin

Ire iren matsalolin da aka gano lokacin kididdigar a wajen rukunonin biyu ( na yan gudun hijira da na mutanen da suka tashi daga garuruwansu zuwa wasu wurare a cikin jahar Difa ) iri daya ne . Daga ciki akwai fada tsakanin kungiyoyin yan tayar da kayar baya, da sace sace da fashi da makami, da yi ma farar hula duka ko azabar da ta shafi gangar jikinsu. Yan gudun hijira sun fi fuskantar ire iren wadannan matsalolin na tsaro. A karshe, baya ga taba lafiyar jikin mutane, rashin takardun tantancewa, da matsalolin rashin rejistar jinjirai na daga cikin kalubalan da aka gano a cikin sansanonin da aka yi ma kididdiga.

Haka lamarin yake wajen rukunonin wasu jinsinan al'uma masu rauni kamar kananan yara,da mata,da tsofaffi,da kuma nakasassu.Kalubalan bayar da kariya da kulawar da aka fi kididdigewa game da yara kanana, sun hada da tsoro mai nasaba da musgunawa ko gallazawar da aka yi musu ko suka ga an yi ma wasu mutane, da kuma musgunawar da aka yi musu cikin iyalansu.Shan miyagun kwayoyi alal misali, an zana shi a matsayin hanyar kauce ma musgunawa. Musgunawa a dalilin jinsi ta karu a dalilin kaurar da mutane suka yi .Ita wannan musgunawar iri iri ce : akwai duka, da musgunawar da ke taba hankali,da da ta tattalin arziki da kuma fyade.Kuma a cewar mutanen da aka tattauna da su yayin aikin kididdigar da aka yi a cikin sansanoni, ire iren wannan musgunawar na da nasaba ne da talauci, da kuma cinkoson da ke akwai a cikin sansanonin yan gudun hijiran da na mutanen da suka bar garuruwansu a cikin jahar ta Difa.Auren wuri da auren gaggawa na daga cikin matsalolin da aka gano a cikin al'uma duk da illolin da suke tattare da su kamar yadda mutanen da aka tattauna da su wajen kididdiga suka tabbatar. Ko da yake wasu matan da aka tattauna da su, sun ce an samu ci gaba wajen matsakaitan shekarun da suka dace a yi wa yan mata aure sakamakon fadakarwar da ake yi, sai dai wasu

yan matan da aka tattauna da sub a su tabbatar da hakan ba. Mutanen da ke fama da wata nakasa ta kabar jikinsu na fuskantar wasu matsaloli na daban a dalilin nakasar tasu.Sun koka musamman da wariyar da ake nuna musu rashin ma'aikatun da suka dace domin taimaka musu. Yan gudun hijiran da mutanen da suka bar garuruwansu, sun gudanar da ayyuka da fusa'o'I da dama domin kyautata ma kansu yanayin tsaro da na rayuwa a inda suke zaune.Tsarin gargajiya da ke akwai a garuruwa na ainahi,kamar tunkarar mai gari ko bulama idan wata matsala ta taso,na ci gaba da taka muhimmiyar rawa wajen shawo kai ko riga kafin tashe tashen hankula , ko a cikin al'uma daya,ko a tsakanin al'umomi .Hakikan duk da cewa karfin ikonsu ya rage biyo bayan kaura da kuma samuwar wasu hukumomi ko ma'aikatu a cikin sansanonin yan gudun hijira, masu garuruwan ko Bulama su ne dai yan gudun hijiran ke tunkara game da duk wasu al'amurran da suka shafe su.Wata fusa'ar da yan gudun hijiran da mutanen da suka bar garuruwansu suka fito da ita, itace ta cuduwa da al'umar da suka tarda maimakon su koma gefe. Hakan na ba su damar samun tsaro da wasu abubuwan more rayuwada ke akwai.Gwamnati ta gudanar da wasu ayyuka na musamman domin karfafa tsaro a jahar ta Difa .Kashi 73 cikin100 na sansanonin mutanen da suka bar garuruwansu suka koma wasu wurare a cikin jahar ta Difa,da kuma kashi 53 cikin 100 na sansanonin yan gudun hijira sun tabbatar da haka yayin kididdigar da aka yi musu.Matakan karfafa tsaron da gwamnati da hukumomin yankin suka dauka sun hada da kara yawan sintirin da jami'an tsaro ke yi, da karfafa tsaro a cikin jahar baki daya.Shi ma aikin bayar da agaji ya inganta,saboda an kyautata rayuwar yan gudun hijiran,an kuma inganta yanayin halin da ake ciki ta fannin ba jama kariya da kulawar da ta dace.Haka zalika a cikin sansanonin an kafa tsare tsare na gargajiya da wadanda ban a gargajiya ba domin riga kafi da shawo kan rigingimu tsakanin jama'a mazauna jahar da baki yan gudun hijira

ko wadanda suka bar garuruwansu. A jimilce daukacin sansanonin da suka taba samun rigingimu, an kafa musu ire iren wadannan matakan riga kafi ko shawo kan rikici.

Jama’an da suka bar garuruwansu suka koma wasu wurare a cikin jahar ta Difa na fuskantar matsalar samun abubuwan more rayuwa.Manya manyan kalubalan da aka tabbatar da yan gudun hijira da mutanen da suka bar garuruwansu suka koma wasu wurare na fuskanta sun hada da samun ruwan sha, da makewaya,da ilmi,da kuma abinci .Wadannan matsalolin sun kara ta’azzara saboda matsalolin tsaron da yankin ke fuskanta,musamman idan ya zamanto wuraren samun ruwan shan,da abinci,ko makarantun ba kusa ga sansanonin suke ba. Saboda haka mutanen da ke son cimma wadannan abubuwan more rayuwar kan fada cikin tsaka mai wuya : ko dai su nemi samun wadannan abubuwan amma fa su tunkari dimbin hadarin da ke tattare da haka,ko kuma su zauna cikin wurarensu masu cikakken tsaron amma ba abubuwan more rayuwar.Wannan zabin dai kan bambanta daga wani rukunin yan gudun hijiran  zuwa wani kamar yadda mutanen da suka halarci tattaunawar kididdigar suka tabbatar.Ta haka ne wasu mata da yan mata suka ce ba su kara tafiya makewaya saboda hadarin da ke tattare da haka,yayin da wasu yaran suka daina zuwa makaranta saboda gudun kada a sace su a cikin makarantunsu,lamarin da yay i kamari a yankin.Amma duk da haka wasu na ci gaba da tafiya neman wadannan abubuwan mure rayuwar duk da hadarin da ke akwai saboda ba su da wani zabi. Alal misali masunta ( masu kamun kifi ) na zuwa kamun kifi a tafkin Cadi duk da cewa akwai kungiyoyin tayar da kayar baya a wurin,haka zalika wasu yara kan yi doguwar tafiya su jenesa domin neman itacen girki , ko kuma wasu yaran kan tafi makaranta duk da barazanar tsaron da ke akwai a yankin. Domin samun abubuwan more rayuwar da kayayyakin abinci, al’umomin da

lamarin ya shafa kan saka kansu cikin wasu ayyuka na assha kamar karuwanci, aikin dole ko tilas, abubuwan da aka tabbatar kananan yara ma na yinsu. Mutanen da suka bar garuruwansu suka koma wasu yankuna a cikin jahar ta Difa da yan gudun hijiran da aka tattauna da su lokacin da aka yi kididdiga,duk sun bada ire iren wadannan misalan.Wadannan ayyukan na assha na kara dagula halin da yan gudun hijiran ke ciki, sannan babban abin damuwa ne ta fannin bayar da kariya da kulawa,kuma lamarin ka iya ta'azzara muddin ba a magance su ba.

## 2. Manufa

Babbar manufar tsarin itace ba yan mata,da samari,da mata da maza,da suka hada da yan gudun hijiran Nijeriya,da yan nijar mazauna Nijeriyar da yaki ya tilasta ma dawowa gida,da kuma mutanen da suka bar garuruwansu suka koma wasu yankuna a cikin jahar ta Difa muhimman hakokinsu na rayuwa, ta hanyar gudanar da ayyukan agaji tun daga farkon tashe tashen hankulan har karshensu.Bayar da kariya da kulawa, ita ce ginshikin ayyukan agaji.Sannan ana fatan duk wasu ayyukan riga kafin kaurar jama'a an gudanar da su.

## Nauyin da ya rataya ga wuyan hukumomi da kungiyoyin agaji

Rukuni ko hadin gwiwar kungiyoyin agaji da ke aiki a cikin jhar Difa shi ne zai kula wajen gudanar da duk wasu ayyukan kariya da kulawar da kungiyoyin agajin za su yi. Musamman zai tabbatar da kungiyoyin agajin sun ba maganar kariya da kulawa matsayinta na ginshiki a cikin ayyukan agaji baki dayansu a kasar Nijar,musamman a cikin jahar Difa.Za atabbatar da hakan ne ta hanyar bi sau da kafa,da bincike, da nazari game da halin da al'amurra ke ciki, da kuma tabbatar da

kungiyoyin agajin sun yi kyakkyawan tsarin ayyukan da za su yi ta fannin kariya da kulawar da za su ba jama'a.

## Manya manyan tsare tsaren ayyukan agaji

## Babban gurin da rukunin kungiyoyin agajin suka sa gaba ta fannin kariya da kulawa

Babban gurin da aka sa gaba shi ne tabbatar da cewa daukacin kungiyoyin agajin sun saka maganar bayar da kariya da kulawa a cikin tsarin ayyukansu. Sannan a rage ma jama'a tsananin kuncin rayuwar da suke ciki ta hanyar karfafa ayyukan riga kafi da shawo kan matsalolin da mutane da fuskanta.

Wannan babban gurin za a tabbatar da shi ta hanyar gudanar da ayyuka da dama da ake iya hadewa a cikin ginshikai 6 wanda kowanensu guri ne na musamman.

**a. Guri na musamman na 1:**Shi ne a karfafa tsarin ayyukan agaji kuma a tabbatar da an saka maganar bayar da kariya da kulawa a cikin daukacin ayyukan agajin da za a yi , hakan zai bada damar inganta kariya da kulawar da ake bayarwa ga yan mata,samari,maza,da mata, da mutanen da tashe tashen hankula suka tilasta ma tserewa suna barin garuruwansu domin komawa wasu wuraren.

**b. Guri na musamman na 2 :** Shi ne kyautata yanayin aikin bayar da kariyar da kulawa ta hanyar yin cikakken nazarin halin da mutanen da suka kauran ke ciki, da yin rejistar kowanensu, da takardun tantancewa ga kowane dan gudun hijira ko wanda yak aura,da kuma karfafa tsarin magance matsalolin da suke ciki.

**c. Guri na musamman na 3 :** Shi ne tsarawa da karfafa tsarin tattarawa da musayar bayanai, da nazarin matsalolin da ake cin karo

da su wajen bayar da kariya, da nuna hanyoyin da suka dace domin daukar nauyin mutanen da ke cikin matsala.Hakan zai bada damar yin cikakken bi sau da kafa na kowane dan gudun hijira har ma abin da ya shafi bas hi damar tunkarar shari'a idan yana jin an ci hakinsa ko an zalunce shi.

**.**Samar da cikakken tsarin bayanai ko labarai da za su taimaka wajen ba mutane kyakkyawar kulawar da ta zo daidai datsare tsaren bayar da agaji na duniya dangance da matsalolin da mutane ke ciki

**.**Kafa tsarin karfafa kwarin gwiwa ga jami'ai na gwamnati da wadanda ban a gwamnati ba ta ta hanyar bas u horo a kan yadda ya kamata su gudanar da ayyukan bayar da kariya da kulawa ga jama'an da suka tagayyara.

**d. Guri na musamman na 4 :**Shi ne karfafa tsarin tafiyar da harkokin sansanonin da aka kafa a cikin gaggawa domin ba al'uma damar daukar nauyin mutanen da suka tagayyara ta hanyar samar da hlin yin hakan,musamman ma kula da matasa a cikin jahar ta Difa.

**e. Guri na musamman na 5 :** Shi ne karfafa ma tsarin riga kafi da shawo kan matsalolin yan gudun hijira, da karfafa ma dukan masu hannu a cikin aikin dawainiya da yan gudun hijira domin inganta aikin da suke yi.Hakan zai taimaka wajen rage fyaden da ake yi ma mata da yan mata

**f. Guri na musamman na 6 :**Shi ne karfafa ma dukan masu hannu a cikin aikin dawainiya da yan gudun hijira na kasa da na jaha domin kyautata aikinsu na riga kafi da shawo kan matsaloli ko biya ma yara yan gudun hijira bukatunsu na rayuwa dangance da ayyukan agajin da ake yi,sannan kuma a tabbatar da an gangara a cikin sauki daga ayyukan agaji zuwa na ci gaba mai dorewa .

A karshe a san da duk da cewa matsalolin tsaro dana hijiran da da jahar Difa ke fama da sun a da tasiri ga ilmin yara, wannan tsari ko fusa'ar dawainiya da yan gudun hijiran bai tanadi kula da sha'anin ilmi ba saboda an kafa wani kwamiti mai kula da ilmi daban da zai kula da maganar.

## 3. Tsarin gudanar da ayyukan agaji :

Bangaren bayar da kariya da kulawa ga yan gudun hijira na daga cikin tsarin ayyukan agaji a cikin jahar Difa,da kuma tsarin ayyukan agaji a cikin jahohin Tilaberi da Tawa.

## 4. Bin ayyukan agaji sau da kafa:

Tsarin bin ayyukan agajin sau da kafa ya dogara ne a kan tarurukan wata zuwa wata da ake yi domin yin nazari a kan yadda ake gudanar da ayyukan agajin da aka tsara,sannan a duba matsalolin da ke hana ruwa gudu da abokan arziki suka bayyana a wajen tarurukan.Matakan da ake dauka domin magance matsalolin, kan iya kasancewa na zuwa a kai kuka wajen hukumomi da abokan arziki ko kuma na samar da kudade da kadarorin tunkarar matsalolin domin ingantawa da karfafa matakan magance su dangance da gurukan da aka sa gaba.Shawarwarin da tarurukan suka bayar za a gabatar ma hadin gwiwar kungiyoyin agaji da ke aiki tare da su ne.Wakilin hadin gwiwar kungiyoyin agaji wajen jagorancin taron, shi ne wakili ko kakakin tsarin bi sau da kafa a cikin rukunin kungiyoyin agajin,sannan shi ne za a dora ma nauyin tsara ayyukan bi sau da kafa tare da hadin gwiwar masu gudanar da ayyukan kariyar jama'a a yankin.

### 5.Bi sau da kafa da auna sakamakon ayyukan da ake yi :

Rukuni ko hadin gwiwar kungiyoyin agaji masu aiki a cikin jahar Difa sun dau alkawalin kafa tsarin bin ayyukan da suke yi sau da kafa domin aunawa su ga in sun cimma muhimman gurukan da suka sa gaba

dangance da tsarin aikin da suka yi,musamman game da ayyukan bayar da kariya da kulawa baki dayanta,da kula da yara, da kuma kula da mutanen da suka kubuta daga azabar fyaden da aka yi musu.

Rukuni ko hadin gwiwar kungiyoyin agaji zai wallafa kammalallen sakamakon ayyukan da kungiyoyin agaji suka yi,da ci gaban da suka samu domin bunkasawa da kyautata muhimmancin aikin bayar da kariya da kulawa a cikin aikin da kungiyoyin agaji key i a cikin kasar Nijar.Saboda haka a lokacin da rukunin kungiyoyin agajin zai gudanar da tarurukansa, za a rika auna sakamakon ayyukan tare da kasancewar dukan masu ruwa da tsaki a cikin ayyukan agajin.Za a duba a tantance Kalubalai,da matsalolin da ke hana ruwa gudu,domin daukar matakan shawo kansu.Za a yi amfani da ma'aunai,da alkaluma domin tantance tasirin da ayyukan rukuni ko hadin gwiwar kungiyoyin agajin ya yi.

**6. Tsarin ayyukan fusa'ar**

Tsarin ayyukan da za a yi, za a makala shi ne ga wannan fusa'ar.A cikin tsarin ayyukan za a saka matsalolin da ake fuskanta wajen bayar da kariya, da ayyuka mafi fifiko da za a fara yi, da sauran ayyukan da za a yi, kowane a rubuta sunan kungiyar da za ta gudanar da shi tare da kayyade lokacin da za ta kamala aikin.

**Rataye na 1( Annex ): Ka'idojin da ake bi**

Wajibi ne a kiyaye da wasu ka'idojin aiki masu dama domin gudanar da ayyukan da za su taimaka wajen cimma gururukan nan na musamman da muka yi bayani can sama.Wadannan ka'idojin aikin su ne za su taimaka wajen tabbatar da cewa aikin bayar da kariya da kulawa na daga cikin muhimman ayyukan agajin da ake gudanarwa a cikin jahar Difa.Haka zalika bin ka'idojin aikin na sa kowane daga cikin masu ayyukan agaji a cikin jahar ta Difa ya san nauyin da ya rataya gare shi.Dukansu na aiki ne ko na kiyayewa ne da matakai ko ka'idoji da suka hada da mutunci,da rishin son rai, yanci da aikata adalci.

Domin haka masu gudanar da ayyukan agajin sun dau alkawulan kiyaye da dokoki kamar haka:

**a )Nauyin da ya rataya ga wuyansu zuwa ga jama'an da ke cikin matsatsi:**

Dangance da nauyin da aka rataya ma kowane daga cikinsu,kungiyoyin agaji wajibi ne su gudanar da ayyukan kuma su sanar da jama'an da suka tagayyara wadanda suke yi ma aikin. Wajibi ne kowa ya sa bakinsa ko hannunsa wajen gudanar da ayyukan da suke yi, kuma ayyukan kariyar da suke yi su yi su dangance da bukatun al'uma.Saboda haka wajibi ne su tabbatar da cewa tsofaffi,da yara, da matasa,da kuma wasu mutanen masu bukatoci daban da na saura sun sa hannunsu ko bakinsu cikin ayyukan da ake gudanarwa domin su. Haka zalika masu ayyukan agaji wajibi ne su rika yin bayani na gaskiya lokaci zuwa lokaci a kan ayyukan da suke yi,sannan kuma su rika tuntubar al'uma da shugabanninta domin sanar da su matakan da suka shafe su,tare da kiyaye sirrin kowane mutum;

**b) Kada su cuta ma al'umar da suke kai ma agaji**

A cikin jahar Difa mai fama da matsalolin tsaro masu nasaba da hare haren yan kungiyar boko haram ,wajibi ne masu gudanar da ayyukan agaji su kiyaye don kada su cuta ma jama’an da suke taimaka ma, su tabbatar da taimakawar suna yinta ne tare da kare jama’an da suke taimaka ma daga duk wani hadari,tare da bada kulawa ta musamman ga mata da yara.Ta hanyar ayyukan da suke yi, masu ayyukan agaji bai kamata su cutar ba, ko su jawo ma farar hulan da ke cikin yankunan da ake tashin hankali wani hadari,ko su lalata muhalli, ko su haddasa tashin hankali a tsakanin al’umomi, ko tsakanin al’umomin da da ma suna cikin tashin hankali.

**c) Aikata adalci da rashin wariya a cikin aikin agaji** :

Manufa guda daya tak ga masu aikin agaji ita ce su ceci rayukan mutane farar hula,su taimaka musu kuma su kare su duk inda suke ba tare da nuna musu wani bambanci ba.Haramci ne ga masu aikin agaji su nuna bambance bambance tsakanin mutanen da suke kai ma agaji.

**d) Samun damar kai agaji ga masu ayyukan agaji :**

Nauyi ne ga gwamnati ta saukaka ma masu ayyukan agaji domin su samu isa wajen jama’an da za su taimaka ma, sannan kuma nauyi ne ga gwamnati ta kare lafiyar jami’an kungiyoyin agaji.Su kuma kungiyoyin agajin, nauyi ne gare su su bada taimakon, kuma su tabbatar da mutanen da ke cikin matsalar ne aka ba taimakon.Wannan agajin ana bayar da shi ne dangance da matakan tsarin bayar da agaji na duniya da kuma ka’idoji ko dokokin bayar da agaji.

**e) Sirri**

Babban guri a nan shi ne tattabar da sirri wajen musayar bayanai da labarai tsakanin masu aikin bayar da agaji a cikin jahar Difa.Yarjejeniyar musayar bayanan da labarai tsakanin masu aikin bayar da agajin ,an rattaba hannu a kanta ne a cikin watan mayu na 2à17.

**Rataye 2 Tasrin saka wasu matakai na musamman a cikin ayyukan yau da kullum na rukunin kungiyoyin agaji a Nijar,tsarin da aka yi a cikin watan mayu na 2à17**

**Manya manyan gururukan da aka sa gaba dangane da hannunta ma gwamnati wasu ayyukan da ya zama wajibi gare ta ta yi su:**

- Karfafa ayyukan bayar da kariya da kulawar da gwamnatin ke yi a cikin gaggawa idan mutane suka kaura a uzurce a cikin kasarsu.
- Kyautata yanayin ayyukan bayar da kariya da gwamnati ke yi,tare da gudanar da taruruka don daukar matakan kare hakin mutanen da suka kaura a cikin kasarsu.

**Gururuka na musamman da aka sa gaba dangane da hannunta ma gwamnati wasu ayyukan da ya zama wajibi ta yi su :**

1.Taimakawa wajen karfafa ma hukumomin gwamnati gwiwa domin gudanar da ayyukan kariya da kula da jama'an da ke cikin matsatsi.

2. Gwamnati ta kyautata yanayin aikinta na bin ayyukan agaji sau da kafa,sannan ta tsare matsayinta na jagorar ayyukan agaji

3. Kai kuka ga gwamnati domin ganin ta yi dokoki na kasa game da kare hakin mutanen da suka kaura a cikin kasarsu . Ma'aikatar ministan shari'a da kare hakin dan adam ce ya kamata ta yi wannan aikin tare da hadin gwiwar dukan masu ruwa da tsaki na jahohi da gundumomi.

4. Kulla kawance tsakanin kungiyoyi masu zaman kansu da abokan arziki masu hannu da shuni irin su hukumar kare hakin dan adam ta kasa , da hukumar raya kasahe ta majalisar dinkin duniya PNUD ko UNDP,da kuma kasashe da kungiyoyi na duniya masu hannu da shuni da ke taimakawa da kudi da kadarori.

AD )1

-Yin taswirar dukan masu ruwa da tsaki a cikin aikin agaji,sannan a karfafa ma masu ruwa da tsaki na kasa,da na jahohi,da kuma na gundumomi kwarin gwiwa.

-A auna karfi ko halin kowace kungiyar kai agaji ta kasa da ta kasa da kasa ( duniya ) a ga in ta iya daukar nauyin ayyukan da ma’aikatar jaha mai kula da kananan yara ke yi a yanzu haka,musamman abin da ya shafi : i ) jagoranci ko shugabancin ayyukan da ake yi, ii ) sa ido ko kuma lura da yadda ake gudanar da ayyukan bayar da kariya da kulawa, iii ) bayar da labarai,da tattara bayanai, musayar bayanai , iv ) nazari, v) kai kuka wajen hukumomi da abokan arziki, vi )wayar da kai ko fadakarwa,da kuma bada horo game da yadda ake gudanar da ayyukan bayar da kariya ga mutanen da suka kaura daga garuruwansu suka koma wasu yankuna, vii ) gudanar da wasu ayyuka a zahiri domin kyautata rayuwar mutanen da suka kaura,kamar yin riga kafin cututuka,kare haki da kyautata rayuwar kananan yara, bayar da shawarwari game da duk wasu zantutukan da sukashafi doka, bayar da magunguna, tattarawa tare da adana takardun da suka shafi aikin bayar da agaji,

- Karfafa ma kungiyoyin farar hula da sauran masu bada kokarinsu a cikin karkara gwiwa a kan aikin da suke yi game da bayar da kariya da kulawar da ta dace gay an gudun hijira

-Yin wani tsari na shekaru da dama game da karfafa gwiwa wanda ya kunshi wata hikima da za ta bada damar auna karfi ko kokarin masu ruwa da tsaki na cikin kasa, game da maganar bayar da kariya ga mutanen da suka kaura a cikin kasa,da kuma tantance matakan shawo kan matsalolinsu

- A zauna a yi nazari tare da juna a kan yadda maganar bayar da kariya take a cikin tsare tsaren ayyukan ci gaba da samar da kudaden gudanarwa ga duk wani mai aikin kai agaji na cikin kasa.

- Yin taswirar masu hannu da shuni da ke iya zuba kudaden gudanarwa ( wadanda ke akwai da wadanda ake sa ran suna iya bayarwa, da tsofin da sabi da kuma wadanda ba a taba tunkararsu ba,domin ayyukan

bayar da kariya,da kyautata rayuwar mutanen da suka kaura suka bar garuruwansu suka koma wasu wurare a cikin kasa. A nan ana iya tuntubar hukumar raya kasashe ta majalisar dinkin duniya PNUD, da bankin duniya, da kuma bankin Asiya mai kula da raya kasashen duniya

- A duba,a tabbatar in ana iya samun amincewar masu hannu da shunin da za su zuba kudaden gudanar da ayyukan,sannan a tabbatar in suna iya taimaka ma masu ruwa da tsaki na cikin kasa ( na jahohi,da na gundumomi ko kananan hukumomi )

- Samar dawata dubarar tattara kudade da za a tallafa ma masu ayyukan agajin da su,kuma idan ta kama a taimaka musu wajen yin tsarin ayyukan da suke son a bas u kudaden gudanar da su

- Dafa ma masu ayyukan agaji na cikin kasa domin su kai kukansu, don a saka nazarin nan da aka yi tare a cikin tsare tsaren ayyukan ci gaba,sannan a yi amfani da wannan nazarin domin samun kudaden gudanarwa

AD2

-Gwamnati ta san nauyin da ya rataya ga wuyanta a cikin aikin jagorancin ayyukan agaji,da kuma nauyin da ya rataya ga wuyanta a cikin rukunin kungiyoyin da ke aikin bayar da agaji

-Wannan aikin na wucin gadi da hukumomin za su yi,wajibi ne ya ci gaba ta hanyar wani tsarin shugabanci da ya hada kowa da kowa

AD 3

- A yi nazarin dokoki, da siyasoshi ko tsare tsaren da ke yin kyakkyawan tasiri ko akasin haka ga aikin bayar da kariya ga mutanen da suka kaura

-A yada dokoki na kasa da siyasoshi ko tsare tsaren da suka shafi aikin bayar da kariya ga mutanen da suka kaura daga garuruwansu zuwa wasu yankuna, musamman mata da yara

-A taimaka ta hanyar tattaunawa tsakanin hukumomi na gwamnati da yan majalisar dokoki domin a cikin kasar ta Nijar a yada yarjejeniyar Kampala ta watan oktoban 2009 wadda ta yi bayani game da agajin da ya dace aba mutanen da suka kaura daga garuruwansu suka koma wasu yankuna a Afrika

-A taimaka wajen karfafa ma duk wasu masu iya gudanar da ayyukan agaji gwiwa don su yi aiki da rukunin kungiyoyin agaji da ke aiki a jahar Difa,musamman ta fannin yada dokokin da suka shafi bayar da kariya ga mutanen da suka kaura

-A saka duk wani aikin da aka yi a kan wata doka ko siyasa a cikin fusa'a da matakan kyautata rayuwar mutanen da suka kaura daga garuruwansu zuwa wasu yankuna cikin kasa

AD4

- A yi aiki da duk wasu tsare tsaren ayyukan ci gaba ( na gwamnati da na ku ngiyoyi masu zaman kansu ) da suka kunshi batun mutanen da suka kaura,ko da suke aiki a cikin yankunan da mutanen da suka kaura ke kokarin kafa sansanoninsu,
- - A yi nazari, a kimanta dokokin kare hakin dan adam da ke akwai a cikin kasa, a karfafa ma hukumomin kananan hukumomi da na gwamnati gwiwa
- A yi amfani da damar saka jarin da ke akwai wajen masu hannu da shuni kamar hukumar raya kasashe ta majalisar dinkin duniya PNUD ko UNDP, Bankin duniya, ko wani can daban domin su tallafa ma banganren hakin dan adam a cikin aikin bayar da kariya

A saka fusa'ar hannunta ma gwamnati wasu ayyukan da ya zama wajibi ta yi su a cikin tsarin ayyuka na kasa baki daya domin shawo kan matsalolin da mutanen da suka kaura ke fama da su

-A karfafa ma tsarin bayar da agji da ke akwai a cikin yankuna wajen tsugunar da mutanen da suka kaura daga garuruwansu suka koma wasu wurare cikin kasa

FIN END

-

-